Takardar gwadi | Nijar | Maris 2012


# Kantin saida kayan aikin gona na garin kawara

Mawallafi : Proje Kapitalizasiyo

## Gabatarwa

Gurin girka kantin saida kayan aikin gona, ba manoma maza da mata damar samun kayan aikin gona na ƙwarai kuma a kusa gare su, musammam ma abun da ya shafi taki , da kuma kawo masu shawarwari domin taimaka masu wajen ciwo kan wasu matsaloli da suka shafi inganta wurin noma da ƙara albarkatun gonakkai .

Kantin saida kayan gona na garin Kawara na cikin kwamin ɗin Dogarawa , lardin Birnin Ƙwanni, Jahar Tawa. A shekarar 2004 ne wasu jam'iyyu uku da suka ƙunshi maza da mata suka girka ta; jam'iyyu su ne: haɗin kai, zaman lafiya da aminci – da ke cikin tarayyar ƙungiyoyin manoman rani na Nijar (FCMN-Niya). Jam'iyyu uku na ƙunshe da mamba 339 a cikinsu akwai macce 60, da suka haɗu a shekarar 2009 domin girka jam'iyya mai suna Daɗin Kowa.




## Waɗanda tsarin ya shafa :

- **Mambobin da ke cikin tsarin nan uku na manoma maza da mata na jam'iyyar Daɗin Kowa, manoma maza da mata waɗanda ba mambobi ba a jam'iyyar**
  Ka'idodin shiga waɗannan jam'iyyun uku su ne : bin umurnin da suka tsaida a babban taro da kuma biyan cikaro – cikaro Saida ma kowane mutum mamba, da wanda ba mamba taki a farashi guda.

- **Abokan hulɗa**
  Da ban hannun babbar ƙungiyar FCMN-Niya, jam'iyyun nan uku, sun yi wata takardar neman taimako don gina masu kantin saida kayan aikin gona, suka ba da gudunmuwarsu don kyautata

kantin saida kayan aikin gona ta filin yin gini, da ɗauko ruwa da ƙasa da kuma sa hannuwansu cikin aikin.

Huldar ƙasar Faransa ta taimaka masu da siminti da kuma kayan aiki irin na ƙasar waje .
Furojen kayan aikin gona na majalisar ɗinkin duniya mai kula da cimaka da noma (FAO) ya ba da buhu 33 na taki « ire ».

A shekarar 2009, furoje mai kula da haɓaka noma da ƙarfafa kantunan saida kayan aikin gona na jam'iyya (IARBIC) ya kawo gudunmawarshi don kyautata kantin saida kayan gona. Game da haka an samu an gyara babban ɗakin, kuma aka gina ɗakin aje magani domin ƙarfafa jari da bada hayar kayan.

A cikin watan satumba na shekarar 2010, kantin saida kayan aikin gona ya samu gudunmuwa ta buhu 70 na taki NPK 15-15-15 daga furojen IARBIC/ISFP (husa'a dangance da hawan farashin cimaka.)

## Hanyar tafiyar da ayyuka

Ana tafiyar da ayyukan kantin saida kayan aikin gona dangance da ƙoƙarin komitin tafiyar da ayyuka ya ƙunshi mambobi takwas (8), da kuma <an bincike guda biyu (2) duka maza ne. Cikinsu mutum biyar (5) sun iya karantawa da rubutawa: mai tsaro da ya samu horo uku dangance da tafiyar da aikin kantin saida kayan aikin gona, magatakarda da mataimakinshi da mai kula da harakokin saye da mataimakinshi. Kafin a kafa wannan kantin saida kaya, mambobi dayawa daga cikin jam'iyyun nan uku sun samu ƙwarewa ta fuskar yaki da jahilci, a fannin gandarin garin Kawara.

## TASIRI

A shekarar 2006, a kan an ba da bashin rabin kayan da furojen kayan aikin gona ya ba da, kuma ba a samu aka tattara duka kuɗin ba, jam'iyya ta gyara kantin da jikka saba'in (70 000 F) ɗin da suka yi saura cikin jarin nasu.

A shekarar 2009, jam'iyyar ta ɗauko wani sabon bashi na 2.122.000 daga wani asusu da ake kira Kokari. Wannan ya ba ta damar bunƙasa wasu ayyukan noman rani da kuma ƙara sayen kayan kantin (musamman ma taki da maganin kashe ƙwari da suka tashi jimillar kuɗi 1.100.000).

Tun daga wannan shekara ne ta 2009 , jarin ya ƙaru, kuma kuɗin saida taki su ma sun ƙaru tsakanin shekarar 2009 zuwa 2011 inda daga jikka ɗari takwas da hamsin da bakwai da dala ɗari da arba'in da ɗaya (857 705 F) a shekarar 2009 har ya kai miliyon biyu da jikka ɗari biyu ba biyar da dala hamsin da tara (2.195.295 F) a shekarar 2010, sannan ya koma miliyon ɗaya da jikka ɗari tara ba ɗaya da dala goma sha takwas (1.899.090 F) a shekarar 2011.

Bayan haka, yawan masu saye maza da mata ya ƙaru inda ya tashi daga mutum 144 zuwa 326 a shekarar 2009 zuwa 2010, kahin ya koma mutum 191 ranar 30 ga watan juli na 2011.

Waɗannan abubuwa suna nuna farin cikin masu saye a cikin kantin saida kayan aikin noma, dangance da ingancin kayan da ake kawowa, bayan haka ana samun ragowar jikka guda (1000 F) kan kowane buhun takin 15-15-15 tsakaninsu da kasuwa.

## Sabin canje- canje da ingantattun hanyoyin cim ma nasara

Waɗansu hanyoyi da ke nuna ingancin Kantin saida kayan aikin gona:

- Yana daga cikin jam'iyya, da ita ma, take ƙarƙashin tarayyar ƙungiyoyi FCMN-Niya, mai ba ta gudunmuwar (horo,odar kaya a jimilce…);
- Kantin saida kayan aikin gona ya ƙunshi sassa dayawa yake ba taki waɗanda suke cikin garuruwa bakwai na kewaye;
- Kwarewa wajen cika girgam daga mai tsaron kantin dangance da horo daban- daban da ya samu,

bayan haka ana balas na kuɗi kowane wata na kantin saida kayan aikin gona a gaban mambobin komitin tafiyar da ayyuka da masu bincike;

- Yalwatar kayan aiki daban- daban da suka haɗa da maganin raya iri, maganin kashe ƙwari, kayayyakin heshe, kayayyakin badawa haya kamar su kwashe da kuma shawarwari da mai tsaro ke badawa;
- Sauƙin saida kayayyakin kanti a dalilin ingancinsu da ragowar da ke akwai wannan ya sa suke samun ciniki;
- Masu sayen kaya suke tsaida lokuttan buɗewa da na rufewar kantin saida kayan aikin gona;
- Kantin saida kaya na da cikkaken asusu na zamani kuma yana da asusu inda da yake kai kuɗinshi a Banki.

## Cikas

- Wani ɓangare na Kantin saida kaya na bisa hanyar wata ƙorama mai kawo ruwa wani lokaci yana kusa da zubewa;
- Bashin da aka ba da a shekarar 2006 domin lalacewar da albasar da aka noma ta yi dangance da ambaliyar ruwa da ta auku cikin gari ya kawo ragewar tafiyar ayyukan kantin saida kayan aikin gona, har ma wani daga cikin bashin ba a samu aka biya shi ba;
- Kantin saida kaya ba ya da wasu ayyuka na daban da suke taɓo shi : jam'iyyar da yake ƙarƙashinta ba ta da mangaza ta ba da kaya bashi tare da jingina, ba ta da gonar gwaji, kuma ba ta da radiyo na karkara. Akwai dai kasuwa ɗaya cikin garin, amma ba ta da yawan jama'a;
- Babu wata hanya mai sauƙin kaiwa a Kantin, hanya ɗaya ce ita ma ba ta da daɗin bi, musammam ma a lokacin damana. Amma ana samun <an kabu-kabu dayawa da ke zirganiya a wajen wannan ke sauƙaƙa kai da kawo a wurin;
- Cikaro-cikaron mambobin a wurin jam'iyya ba su shiga sosai wannan ko ya danganta da yanayin damana;
- Takin da ake yin tanadi kullum ba ya isa kuma lokaci zuwa lokaci ana rasa shi ne ma;
- Ana iya samun hatsarin cin kuɗi sabili da rashin hakunta waɗanda suka ƙi biyan bashin da suka ɗauka wajen kantin;
- Mata ba su samun kaya ko wasu ayyuka ta hanyar kanti don ba su da gona.

## Gano ƙuraƙurai

Nazarin wannan husa'ar da kuma bayanai da muka samu, na ba mu damar mu riƙe waɗannan darussan :

- Shirya da aje kayan da ke akwai wurin da ya dace tare da an liƙa hotunan da aka ba kanti;
- Tafiyar da jewaya a kowane lokaci domin diba irin halin da gine- gine suke ciki, don kawo gyara tun da wuri;
- Yanke shawara kan albashin da za a ba mai tsaron kanti don a tabbatar da zamanshi cikin kantin (tun da aka buɗa kantin, so guda aka ba shi jikka biyar (5000 F);
- Ba <an bincike cikkaken horo domin su samu su tafiyar da aikinsu yadda ya kamata;
- Ciwo kan wasu masu hannu da shuni bisa ga kyautar da suke badawa ta iri da kuma taki daga wani bangare na FAO ko kuma takin da ma'aikatar magajin gari ke badawa bashi ga wasu garu-ruwa.
- Zaɓen filin da ya dace ga gina kanti, tare da ban hannu ma'aikata mai kula da ayyukan gine-gine cikin karkara.

## Dorewar ayyukan

Ayyukan Kantin saida kaya na garin Kawara na iya ɗorewa dangance da kasancewarshi cikin wuri wanda ake da buƙarta taki sosai. Amma yana buƙatar a ƙarfafa tsarinshi da aikinshi domin cim ma ɗorewarshi. Waɗannan abubuwa sun haɗa da :

- Bin ƙa'iodin da aka tsaida bisa ga kantin saida kayan aikin gona domin guje ma kurakuran da aka fuskanta can baya waɗanda suka haɗa da cin kuɗi da kuma ba da bashi;
- Yin amfani da radiyo na Dogarawa domin isar da labaru bisa kan amfani da kayan aikin noma da kuma inda ake samun su, don ba mai saye hamzari;
- Ƙarfafa gudunmuwar masu hannu da shuni domin samun wasu sabin horo zuwa ga mambobin komitin tafiyar da ayyuka na kantin saida kayan aikin gona (tanadin tafiyar da ayyukan, cikon girgam, nuna amfain taki, da kuma horo ta ɓangaren yaƙi da jahilci).

Capitalisation
Projet Capitalisation (FAO Niger)
BP 11246 Niamey
Tel + 227 20 72 33 62
km-gender@fao.org
www.fao.org/knowledge/km-gender/capitalisation-bp/fr

IARBIC
Projet Intensification de l'Agriculture par le Renforcement des Boutiques d'Intrants Coopératives
FAO BP 11 246 Niamey, NIGER
Tel + 227 20 37 32 36
contact@iarbic.net www.iarbic.net